# Littafi mai Tsarki na yara

**Ke gabatar da**

# Sama'ila, Dan Hidimar Allah



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Lyn Doerksen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

Hannatu mace ce mai kirki, ta auri Elkana, mutumin kirki. Dukansu sun yi wa Allah sujada suna aikata nagarta ga mutane. Amma akwai abin da Hannatu ba ta da shi a rayuwarta. Tana so ta sami yaro. Oh, ina misalin hanzarin ta sami jariri! Ta yi ta jira, tana addu'a tana sa rai tana jira na lokaci. Babu yaron da ya zo.





**Kowane shekara, Hannatu takan tafi ta yi sujada a haikalin Allah.  Wani shekara sai ta yi wa Allah alkawari cewa in ya ba ta da namiji, za ta ba wa Allah yaron ya yi masa hidima har abada.**



Eli tsohon Firist ya hange Hannatu tana addu’a. Yana tuna nin watakila Hannatu ta bugu ne da ruwan inabi saboda ya gan leben bakinta yana motsi amma bai ji kalmomi suna fita ba. Eli ya yi mata fada.



Amma Hannatu ta gaya wa Eli addu’arta na neman yaro da kuma alkawarinta ga Allah. “Tafi cikin salama.” Eli ya amsa. “Kuma Allah na Isra’ila ya biya miki bukatanki wanda kika roka daga gareshi.” Kalmomin Eli suka ba ta bege.

**Ba dadde ba sai farin ciki ya cika zuciyar Hannatu. “UBANGIJI ya tuna da ita” ya kuma amsa addu’arta. Da ita da Elkana suka sami yaro wanda suka ba shi suna Sama’ila. (mai ma’ana “Allah ya ji”). Amma ko Hanantu za ta tuna da UBANGIJI da alkawarinta gareshi?**





**Hannatu ta bar zuwa haikalin kowace shekara. Oh, aminiyata! Ta karya alkawainta ga Allah kenan? A'a, Hannatu tana jira ne sai Sama'ila ya yi girma ya kai yadda zai zauna da Elai yana taimake shi a tentin da hidimar Allah. Sa'an nan ta kawo shi a tentin.**



**Allah ya daukaka amincin Hannatu mai girma.  Bayan Sama'ila, Allah ya ba ta 'ya'ya maza uku da 'yan mata biyu.  Kowane shekara Hannatu takan tafi tentin domin ta yi wa Allah sujada – ta kuma kai sabon rigar ta yi wa Sama'ila.**



Ba Sama'ila ne kadai mataimakin Eli ba. 'Ya'yan Eli Hofni da Finehas, su ma sun yi aiki a wurin. Amma ba su daukaka sunan Allah ba ta wurin mugayen ayyukan da suka aikata, kuma sun ki su canja duk da rokon da babansu Eli ya yi. Yakamata da Eli ya kore su daga yin aiki a tentin. Amma bai yi ba



**Wani dare, Sama'ila ya ji murya na kiransa. Saurayin yana gani kamar Eli ne yana kira. "Ga ni nan," ya ce. "Ban kira ka ba," Eli ya amsa. Wannan ya faru sau uku. Sai Eli ya sani cewa Allah yana so ya yi magana da Sama'ila ne.**



**Eli ya gaya wa Sama’ila, “Idan ya kira ka, dole ka ce, ‘Yi magana UBANGIJI, gama bawanka yana ji.’” Allah kuwa ya kira, sai ya ba wa Sama’ila sako mai muhimmanci.**

**Da safe Eli ya kira Sama'ila. "Mene ne abin da UBANGIJI ya fada maka?" ya tambaya. Saurayi Sama'ila ya gaya masa kome da kome. Mugun sako ne – Allah zai hallakar da duka iyalin Eli saboda Hofni da Finehas sun yi mugunta sosai.**



**Gargadin Allah ya zama gaskiya. Lokacin yaki tsakanin Isra'ila da Filistiyawa, mugayen 'ya'yan Eli guda biyun nan suka jagorance yakin rike da Akwatin Allah a gaban sojojin Isra'ila. Abokan gaban suka kwace Akwatin sai suka kashe Hofni da Finehas tare da Isra'ilawa masu yawa. Sa'ad da Eli ya ji labarin, sai ya fadi daga kujerarsa, ya karya wuyansa, ya mutu rana daya da su.**



**Akwatin ya jawo wa Filistiyawa matsifa. Suka sa shi a haikalin Dagon, allahnsu na karya. Da safe, gunkin Dagon ya fadi da fuska a kasa. Filistiyawa suka ta da shi daga kasa – amma washegari kuma sai ga shi a kasa. A wannan karon Dagon ya faffashe.**





**Ciwo da mutuwa ya bazzu ko'ina a tsakanin Filistiyawa. Domin su sani ko Allah yana hukunta su ne, sai Filisitiyawa suka sa shanu biyu su ja Akwatin. Amma suka bar yaran shanun a wurinsu. "Idan shanun sun haura zuwa Isra'ila, sai suka bar 'ya'yansu, za mu sani cewa Allah ne ya aikata wannan," suka ce. Haka shanun suka haura!**



**Sai Sama’ila, wanda yanzu ya yi girma, ya yi magana da duka mutanen Isra’ila. “Idan kuka dawo wurin UBANGIJI da dukan zukatanku… Zai kubutar da ku daga hannun Filistiyawa.” Mutanen suka yi biyayya ga annabi mai aminci na Allah. Hannun Ubangiji ya sauka a kan Filistiyawa duka kwanakin Sama’ila.**

# Sama'ila, Dan Hidimar Allah

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**1 Sama'ila 1-7**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

# KARSHE

17

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**